

# EARL

Shirin EARL na aikin taimakawa tsofaffin da aka ci zarafin su ba dare ba rana a yankin Calgary da wasu yankuna ta hanyar bada bayanan da suka kamata domin kai musu dauki.

Za ku iya kiran layin wayar EARL domin neman karin bayani ko samun mafaka ga wadanda ke fuskantar cin zarafi musamman dattijai, ko yin tambayoyi game da wannan matsala.

**403-705-3250**

FOUNDATION

unison™


**Calgary**

Kerby Centre

*1133–7 Avenue S.W.*

*Calgary, AB T2P 1B2*

*(403) 265-0661*

**UnisonAlberta.com**


Alberta

Seniors Community & Social Services


*Charitable # 11897 9947 RR0001*


unison

At Kerby Centre

## TAIMAKO GA DATTIJAN DA AKA CI ZARAFIN SU

---

## Elder Abuse Supports

## Hausa Translation



# Elder Abuse Shelter

Cibiyar mu na samar da mafaka mai kyau ga tsofaffin ko dattijan da suka tsere daga gidajensu saboda cin zarafin su da ake yi.

Muna da gadojin kwantar da wadanda aka ci zarafi guda goma sha hudu (14) da gado daya (1) na bada agajin gaggawa domin nunawa 'yan sanda da sauran hukumomi. Tsawon kwanakin casa'in (90) wato wata uku (3) mutum zai kwashe a cibiyar. Sannan muna maraba da maza da mata a koda yaushe.

Tun bayan fara samun wannan matsala, cibiyar nan ta EARL na aiki tukuru, sannan a wani lokaci muna komawa da wasu tsaffin har gidajen su.





Haka nan a lokacin da dattijan da aka ci zarafin su ke zaune a matsugunin, suna samun ilimi mai inganci da nishadantar da su, da basu tallafin kudi da nema musu gidaje, da tura su wasu wuraren da za a taimaka musu da dai sauran su.

Sannan muna taimakawa wadanda wannan matsala ta shafa na tsawon wata goma sha biyu (12) daga bisani mu koma da su cikin al'ummomin da suka fito.

# NAU'IN CIN ZARAFIN TSOFAFFI/DATTIJAI

### KUDI

Amfani da dukiya, kudi ko kadara ta haramtacciyar hanya ko hanyar da bata kamata ba don cin zarafin su..

### DAMUWA

Cusa musu bakin ciki ko damuwa ta hanyar kalamai marasa dadi ko wani yanayi.

### A JIKI

Yin amfani da karfi har a yi musu rauni ko nakasa su.

### WATSI DASU

Yin watsi da su ko kin samar musu da ababen da suke bukata na rayuwa.

### GUJE MUSU

Kaurace musu daga mutumin da ya kamata ya kula da su.

### LALATA

Cin zarafin su ta hanyar lalata kowace iri ce.